Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.23 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Gurbin Namun Daji, Tsuntsaye, Da Kwari A Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Sakina Adamu Ahmad**

Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya., Jami'ar Jihar Sokoto

**Corresponding Author: Sakina Adamu Ahmad** Sakeena6060@gmail.com
09031497755

**Tsakure**
Kiɗa da waƙa a ƙasar Hausa wani ginshiƙin abu ne da aka aiwatarwa domin ilmantarwa ko sadarwa ko nishaɗantarwa ko bayar da wata gudummuwa ta musamman. Kusan a ce kiɗa ya yi ruwa ya yi tsaki, ya durmiya sosai a cikin rayuwar Bahaushe, musamman rayuwar da ta danganci zamantakewa da sana'o'i da bukukuwa da lokutan shaƙatawa. Akwai waƙoƙin baka da yawa waɗanda suka danganci fuskoki daban- daban tun daga na farauta da yaƙe- yaƙe da na Sarakuna, da na masu sana'o'in gargajiya da na 'yan kasuwa wato attajirai da na masu Jaruntaka da na Sojoji da na ma'aikatan Gwamnati ko wata Hukuma da na Malamai bisa fannoninsu mabambanta da na dabbobi da tsuntsaye da ƙwari da gulabe da gariruwa har zuwa ga waƙoƙin yunwa da fari da na ɓarayi da na 'yan caca da na soyayya da sauransu. Ashe ke nan waƙoƙin baka na Hausa sun yi ruwa da tsaki a ko'ina cikin ɓangarorin rayuwar Hausawa. Duk wani abu da ya shafi fasahar bayyana nagartaccen rayuwa ta mutum da kuma Al'umma wadda ta shafi duniya da wadda ta shafi Lahira tana nan jibge cikin waƙoƙin baka na Hausa. (Gusau, 2014). Alhaji Kassu Zurmi yana ɗaya daga cikin mawaƙan baka na Hausa, wanda Allah ya bashi basira da hazaƙa da fasaha da hikimar naƙaltar harshen Hausa da adabi da abin da ya shafi al'adun Hausawa tun daga sana'a da muhalli da haihuwa da kuma sunayen abubuwa na dabbobi da ƙwari da tsuntsaye da ke cikin duniya baki ɗaya. Wannan muƙala za ta dubi gurbin muhalli na Dabbobi da ƙwari da tsuntsaye da ke cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi. Kuma za a kawo taƙaitaccen tarihin shi mawaƙin, da kuma nuna hanyoyin da aka bi domin tattara wannan bincike da aka yi. Haka kuma, muƙalar za ta kawo sakamakon binciken da kuma kammalawa daga ƙarshe.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa:

Kiɗa da waƙa a ƙasar Hausa wani ginshiƙin abu ne da aka aiwatarwa domin ilmantarwa ko sadarwa ko nishaɗantarwa ko bayar da wata gudummuwa ta musamman. Kusan a ce kiɗa ya yi ruwa ya yi tsaki, ya durmiya sosai a cikin rayuwar Bahaushe, musamman rayuwar da ta danganci zamantakewa da sana'o'i da bukukuwa da lokutan shaƙatawa.

Akwai waƙoƙin baka da yawa waɗanda suka danganci fuskoki daban- daban tun daga na farauta da yaƙe- yaƙe da na Sarakuna, da na masu sana'o'in gargajiya da na 'yan kasuwa wato attajirai da na masu Jaruntaka da na Sojoji da na ma'aikatan Gwamnati ko wata Hukuma da na Malamai bisa fannoninsu mabambanta da na dabbobi da tsuntsaye da ƙwari da gulabe da garuruwa har zuwa ga waƙoƙin yunwa da fari da na ɓarayi da na 'yan caca da na soyayya da sauransu. Ashe ke nan waƙoƙin baka na Hausa sun yi ruwa da tsaki a ko'ina cikin ɓangarorin rayuwar Hausawa.

Duk wani abu da ya shafi fasahar bayyana nagartaccen rayuwa ta mutum da kuma Al'umma wadda ta shafi duniya da wadda ta shafi Lahira tana nan jibge cikin waƙoƙin baka na Hausa. (Gusau, 2014). Alhaji Kassu Zurmi yana ɗaya daga cikin mawaƙan baka na Hausa, wanda Allah ya bashi basira da hazaƙa da fasaha da hikimar naƙaltar harshen Hausa da adabi da abin da ya shafi al'adun Hausawa tun daga sana'a da muhalli da haihuwa da kuma sunayen abubuwa na dabbobi da ƙwari da tsuntsaye da ke cikin duniya baki ɗaya. Wannan muƙala za ta dubi gurbin muhalli na Dabbobi da ƙwari da tsuntsaye da ke cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi. Kuma za a kawo taƙaitaccen tarihin shi mawaƙin, da kuma nuna hanyoyin da aka bi domin tattara wannan bincike da aka yi. Haka kuma, muƙalar za ta kawo sakamakon binciken da kuma kammalawa daga ƙarshe.

## 2.0 Tarihin Alhaji Kassu Zurmi:

An haifi Kassu a wani gari da ake kira Magarya kamin daga bisani ya dawo a ƙauyen Kadawa ta ƙaramar Hukumar Zurmi da ke cikin Jihar Zamfara, a daidai shekara ta 1910. Sunan mahaifinsa Amadu, sunan kakansa kuma Malam Gandau Dumfawa. An yi masa laƙabi da suna Sarkin Fawa Gandau, sunan mahaifiyarsa "Maimuna" wadda ake yima laƙabi da suna Kande 'Yar Gidan Goga.

Sunan Kassu na yanka shi ne Abubakar. Dalilin yi masa wannan laƙabi na Kassu shi ne saboda an haife shi ne a ranar Lahadi kasuwar Dauran, shi ya sa aka yi masa wannan laƙabi watau Kassu kalma ce ma'anar wai mai kasuwa. Asalin Kassu an ce Bagobiri ne, saboda kakanninsa ne Gobirawa. Sun taso daga ƙasar Gobir a wani gari da ake kira Kurawa suka yaɗa zango a wani gari da ake kira "Dumfawa" ta ƙaramar Hukumar Zurmi. Daga nan sai kuma suka tashi daga garin "Dumfawa" suka koma garin "Magarya". Daga garin na "Magarya" kuma suka matsa zuwa wani ƙauye da ake kira "Kadawa" watau "Kwata" duk a cikin ƙaramar hukumar mulki ta Zurmi. Kassu ya nuna haka a cikin waƙar Nomau inda yake cewa:

> "Uban balinɗo, shi ya isheni har Kadawa".

Wannan ya nuna mana cewa shi mutumin Kadawa ne. Kassu Zurmi bai sami damar yin karatun boko na zamani ba, amma ya taɓa karatun Alƙur'ani da sauran littattafai na fiƙihu. (Gusau, 2005) a maƙera ta malan Ladan na garinsu.

Gado, Kassu Zurmi ya gadi kiɗa ne a wajen mahaifinsa. Kassu ya fara bin mahaifinsa wajen kiɗan tun yana yaro ƙarami. Bayan koyon kiɗan da yake yi daga wajen

mahaifinsa ya taɓa kiɗan Duma zaune. kiɗan noma, kiɗin bori, fawa, farauta, da ɓarayi, amma bai mayar da hankalinsa sosai a kansa ba kamar na tauri, shi dai kiɗan ya gada, ya taras ubansa yana yi don haka ya himmatu a kansa, har Allah ya bashi rabo mai yawa a ciki.

A matsayinsa na makaɗin farauta da 'yan tauri ba wai gidajensu kawai yake bi idan suna ko biki ya kama ba, a'a tare dashi ake zuwa dajin farauta, duk abin da aka yi na farauta a gaban sa, ba wani mai bashi labari ra'ayul ainu ne shi. Shi kansa a wasu ɗiyan waƙoƙinsa ya nuna cewa da shi ake zuwa farauta dubi abun da yake cewa:

> "Tahiya makoɗa ko dajin kuna,
> Sa'annan kowaj ji 'yan kalanguna na Jaji na'amadu,
> Sai ɗa da ɗa ka kai nama daji.
> (Waƙar Katakare Jabanda). (Gusau, 2005:225- 226)

Kassu Zurmi yana amfani da kalangu a matsayin abin kiɗansa. Kassu ya yi nau'o'in kaɗe- kaɗe a matsayinsa na makaɗin kalangu. Daga cikinsu akwai kiɗan noma, kiɗan farauta da 'yan tauri, sai kiɗan ɓarayi da 'yan caca.

Kassu Zurmi ya yi aure cike da zuriya mai yawa, ya bar matan aure huɗu waɗanda suka haɗa da: Sa'adiya (Yaya), Jawairiyya (Auta), Aishatau (Karɓa), da Zainab (Abu). Haka kuma, Allah ya azurta shi da 'ya'ya da yawa. Ya bar kimanin ɗiya goma sha biyu shidda maza, shidda mata. Maza sun haɗa da: Umaru ƙaho, Usman, Sani ɗan Gabci, Muhammadu Namakka, Malam Aliyu, da Rabi'u. A halin yanzu uku na raye, uku sun rasu. Waɗanda suka rasu su ne: Umaru ƙaho, Usman, da Sani ɗan Gabci. Waɗanda ke raye su ne: Muhammadu Namakka, Malam Aliyu, da Rabi'u. 'Ya'yansa mata akwai Manga, Salamatu, Raula, Balaraba, Mardiyya da kuma Nana Asma'u, wadda ita ce Auta. Cikin 'ya'ya mata biyu sun rasu, huɗu ne na nan raye, suna aure a gidajen mazansu. Su ne: Raula, da Balaraba, da Mardiyya da Nana Asma'u. (Hira da jikansa, Murtala Usman, 18-12-2024).

Daga cikin manyan 'ya'yansa ne, Umaru ya zama makaɗin Tauri, kusan shi ne mai gadonsu. Amma shi ɗaya ɗan nasa Usman sai ya kama hanyar almajiranci inda ya yi karatun allo da na ilimi. Yanzu haka zauren gidansu ne ya mayar makarantarsa ta allo yana koyar da yara karatun allo.

Kassu Zurmi ya rasu bayan wata rashin lafiya da ya yi har ya kwanta asibitin Gwamnati na Gusau a 1987.

## 3.0 Dabarun Gudanar da Bincike

Aikin bincike irin wannan yana buƙatar a bi hanyoyin da suka dace don a sami, bayanai ingantattu waɗanda kan wadatar da jama'a su sami natsuwa a kan abubuwan da binciken ya haifar. Babban hanyar da aka bi domin tattara bayanai a wannan aiki ita ce, ta sauraren waƙoƙin Kassu Zurmi waɗanda ya yiwa gwazansa daban- daban don zaƙulo wuraren da yake ambaton sunayen dabbobi da ƙwari da kuma tsuntsaye daban- daban a cikin waƙoƙinsu. Bayan wannan hanyar akwai wasu hanyoyi da aka bi aka yi amfani da su waɗanda suka haɗa da ziyartar wasu ɗakunan karatu don samun aikace- aikacen da wasu magabata suka yi maimai kuma a sami ƙarin haske a kan abin da ake sa a gaba. Sannan kuma an tattauna da wasu masana da wasu manazarta da wasu ɗaiɗaikun jama'a waɗanda suka san Kassu Zurmi da kuma waƙoƙinsa. Haka kuma, an zanta da wasu ɗalibai a kan wannan batu, wannan ya ba da ƙwarin guiwar tafiyar da aikin kamar yadda ya dace.

**4.0 Gurbin Kwari, Dabbobi, da Tsuntsaye a Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi**

Alhaji Kassu Zurmi shahararren mawaƙi ne na maza. Inda bai yiwa kowa waƙa sai matcata. Watau 'yan farauta da 'yan Tauri da kuma ɓarayi. Waƙoƙin 'yan tauri matciyata, su ne suka fi do da Kassu Zurmi a fili, musamman waƙar Nomau na Magarya da ta Shayi ɗan gidan Labbo. (Gusau, 2005).

Kassu Zurmi mawaƙi ne wanda Allah ya hore ma iya shirya waƙa cikin hikima da fasaha wadda Allah ya bashi. Kuma ya yi waƙoƙi da dama, a cikin su ne ya ke amfani da sunayen dabbobi da ƙwari da kuma tsuntsaye, domin ya koɗa ko ya zuga Gwarzonsa. Kassu ya yi amfani da gurare daban- daban yana ambatar waɗannan abubuwan a cikin waƙoƙinsa. Misali, a cikin wata waƙa yana cewa:

Jagora: Nik kwan Wagini garin Ɗan'Ani,
: Inda ba a ƙaryar ***Giwa,***
: Yaro in ka yi gardama a ja ka a kai ka,
: In ba Giwad dawa ba Giwad dawa.
( Kassu: Ibrahim Twasshi Birnin Magaji)

A nan Kassu ya ambaci sunan wata dabba da ke daji, watau Giwa. Hausawa na cewa, "Giwa Bukka Daji", watau manyan dawa ke nan.

Sai kuma a cikin wata waƙar ya sake faɗin ko kawo sunan wata dabbar inda yake cewa:

Jagora: Ga ni ina kuka,

: Ga ***Gunzu*** na rasa mai Yamman.

(Kassu: Waƙar Garugaru)

Idan muka lura a nan ma, Kassu ya ambaci Gunzu a matsayin wata dabba da ta haɗa faɗa tsakanin mafarauta.

Haka kuma, a cikin wata waƙar ya sake faɗin ko kawo sunan wata dabbar inda yake cewa:

Jagora: ***Kura*** ta riga ***Kare*** kai ga asirai,
: ***Shaho*** ya riga su ya shanye mazaizai.
(Kassu: Ibrahim Shaho)

A nan mun ga cewa ya kawo mana wasu sunayen dabbobi da tsuntsaye a cikin ɗiyan wannan waƙa tasa. Wato Kura, da Kare dabbobi sai Shaho, shi kuma tsuntsu.

Wani misali kuma Kassu na cewa:

Jagora: ***Kura*** bata cin ***Kada*** ko ta iske ya mutu,
: Ko wuri ya yi kumburi,
: Don ta yadda ko hwata ***Jakki*** baya tamnuwa.
(Kassu, Namakka Ɓoko)

A nan mun ga muhallin da Kassu ua kira wasu dabbobi da ƙwari. Watau Kura da Jakki da kuma Kada, wanda shi ne ƙwaron ruwa ko dabbar ruwa.

Har ila yau, mun ga wasu wurare da Kassu Zurmi ya kawo sunayen Tsuntsaye, a cikin wasu ɗiyan waƙoƙinsa, inda yake cewa:

Jagora: Mun sha ʻyan na lutsa mun sha mai,
: Mun sha ***Zabbi*** ga ɗan gidan Labbo.
(Kassu: Shayi Ɗan Gidan Labbo)

Jagora: Albarkacin ***Kaza*** ƙadangare,
: Kan sha ruwan kasko.
(Kassu: Baƙo Karen Buwai)

A nan mawaƙin ya ambaci tsuntsaye da ƙwari,ʻYan na Lutsa, da Zabbi. Da kuma Kaza, sai wani ƙwaro, wato ƙadangare.

A ci gaba da kawo gurabun tsuntsaye a cikin wasu ɗiyan waƙoƙin na Kassu mawaƙin ya kawo sunayen wasu tsuntsaye a cikin ɗiyan waƙoƙinsa, inda yake cewa:

Jagora: Can tana ta ƙotonta na Abu,
: Yabbiɗo dutci,
: Yad diba, yad diba,
: Yad diba bai ga inda ta hau ba,
: Ashe ko tsuntsayen daji suna da azanci,
: Ko da ya yadda dutcin nan ya wuce,
: Sama ya sari gargare ukku,
: Sai tac ce bari dai mui mai magana,
: Kahin dai ya gane dutcin can na gane shi na tashi,
: Ko gwallo, ko gwallo,
: Ko gwallo inji ***Kurciyar*** gamji,
(Kassu: Shayi ɗan Gidan Labbo)
Wani misalin:

Jagora: Na zo gonata sassabe,
: Sai nijji jawabin ***Kurciya,***
: Tag gani tac ce Kas- kado Kas- kado,
: Kas- kado Kas- kado Kas- kado,
: Ni ɗauki dutsi nat taho,
: Niz zaka jihwar ***Kurciya,***
: Tacce Kassu har hwa ka watce man gida.
(Kassu: Janbiri)

Haka kuma, a wasu ɗiyan waƙoƙin mun ga Kassu Zurmi ya kawo sunayen wasu ƙwari a cikin waƙoƙin nasa inda yake cewa:

Jagora: ***Rina*** mai niyyar mugunta,
: Mai ɗakin mugunta,
(Kassu: Nakwando)

Wani misalin yana cewa:

Jagora: ***Kura ƙuda*** mai ladda na Garba,
: Gandau na dariya yaka ɓanna.
(Kassu: Labbo Na Amadu)

A cikin wasu ɗiyan waƙa mawaƙin na cewa:

Jagora: ***Kusun*** ɗaka mai jimirin ɓaci,
: ***Ɗanburgu*** mai hwarin bindi,
: ***Cinnaka*** Sherinka ya ɓaci.
(Kassu: Mamman Na Jangebe)

Ga wani misali a ɓangaren ƙwarin kamar haka:
Jagora: Garin kowa na da nashi,
: Shi ab ba nakai nai,
: ***Keya*** mai sa ʻyan soshe- soshe.
: ***Tcatctceku*** mugunta ki cikin ruwa ta ke,
(Kassu: Nakwando)

Ga wani misali kamar haka:

Jagora: Kada ku biye bakin ***Tunku***
: Mai bi ɗamma dangi wahala.
(Kassu: Aikau)

Tunku wata dabba ce ta daji mai yawan yin tusa (rihi) mun ga cewa Kassu ya kawo shi a cikin ɗiyan waƙarsa ta Aikau.

A wani misalin ƙwari a cikin waƙoƙin nashi ya ƙara ambatar Sabro a cikin waƙarsa, inda yake cewa:

Jagora: Makaranta na gyara ɗan kowa,
: Amma ba ta gyara ɗa nai ba,
: Shi a ***Sabro*** mai halin banza.
(Kassu: Waƙar Ɗangangan karen ɓalla)

A taƙaice waɗannan bayanai da muka kawo a sama, su ne misalan gurbin ƙwari da dabbobi, da kuma tsuntsaye a cikin wasu waƙoƙin Alhaji Kassu Zurmi da aka kawo a cikin wannan muƙala da aka gabatar.

## 5.0 Sakamakon Bincike

Wannan aikin bincike ya gano wasu wurare daga cikin waƙoƙin makaɗa Kassu Zurmi da aka ambato sunaye wasu dabbobi da ƙwari da kuma tsuntsaye.

Sakamakon wannan binciken ya gano cewa, sunan Alhaji Kassu Zurmi na yanka, shi ne Abubakar Amadu. A ci gaba da sakamakon wannan bincike an gano cewa Kassu Zurmi mawaƙi ne mai fasaha da kuma balaga, da iya ƙulla waƙa da azanci.

Wannan binciken kuma ya gano cewa, Kassu Zurmi yana cikin rukunin makaɗan maza. Saboda kama da ʻyan Tauri da ʻyan farauta da ɓarayi su yake yi wa waƙa.

**6.0 Kammalawa**

Muna godiya ga Allah maɗaukakin Sarki wanda ya nufe shi da ganin na kammala wannan binciken wanda ya kalli Gurbin dabbobi da ƙwari da kuma Tsuntsaye, a cikin waƙoƙin makaɗa Alhaji Kassu Zurmi. Wannan muƙala ta yi ƙoƙarin bayyana ire- iren dabbobi, da ƙwari, da tsuntsaye da Kassu Zurmi ya yi amfani da su a wurare daban- daban a cikin wasu ɗiyan waƙoƙinsa. Binciken ya kawo gabatarwa sannan ya kawo taƙaitaccen tarihin shi mawaƙin, haɗi da bayyana hanyoyin da aka bi domin ganin wannan binciken ya kammala. Sai aka kawo sakamakon binciken. Daga ƙarshe sai aka kuma kammala.

**Manazarta**

Bunza, A.M. (2009) Narambaɗa. Lagos: Ibrash Islamic Publication Centre L.T.D.
Gusau, S.M. (2005) Makaɗa da Mawaƙan Hausa. kano: Benchmark Publishers Limited.
Gusau, S.M. (2003) Jagoran Nazarin Waƙar baka. Kano: Benchmark Publishers Limited.
Gusau, S.M. (2009) Diwanin Waƙoƙin Baka: Zaɓaɓɓen Matani Na Waƙoƙin Baka na Hausa. kano Nijeriya: Century Research and Publishing Limited.
Magaji, A. (2016) Kassu Zurmi Da Waƙoƙinsa. Ibadan: Spectrum Books Limited.
Umar, M.B. (1982) Waƙoƙi Don Yara. Zaria: The Northern Nijeriya Publishing Company.
Yahya, A.B. (2014) Salo Asirin Waƙa. kaduna: Fisbas Media Services.

**HIRA**

Hira da Umaru Kaho, Ranar Lahadi, 20/6/2025
Hira da Malam Yahaya Sarkin Makahin Zurmi. Ranar 14, ga watan 3, 2022.
Hira da Malam Aliyu Kadawa, Ranar 3/5/2017.
Hira da Alhaji Mande Sangamawa, Ranar 3/5/2017.